Duk wanda ya yi girman kai a cikin Zuciyarsa, kuma yake takama a Tafiyarsa, zai gamu da Allah yana fushi da shi

Daga Abdullahi Bn Umar -Allah ya yarda da su- ya ce: Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Duk wanda ya yi girman kai a cikin Zuciyarsa, kuma yake takama a Tafiyarsa, zai gamu da Allah yana fushi da shi"

[Ingantacce ne] [Al-Hakim Ya Rawaito shi - Ahmad ne ya rawaito shi]

Hadisin yana nuna Zargin girman kai da kuma daga kai, kuma wannan daga kan a tafiya ne ya Takama a cikinta, a cikin Tufafinsa da kuma Maganganun su, kuma a cikin kowane Al-amarinsa, kuma duk wanda ya Kasance wannan ne halinsa don girman kan yana kudurcewa a cikin ransa cewa shi Babba ne to ya cancanci a girmama shi sama da yadda wani ya cancanta to cewa shi Allah zai jefa shi cikin Wuta a ranar Al-kiyama kuma yana fushi da shi

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5513